# Fiqihun ibada a cikin hotuna

Karantar da hukunce-hukuncen musulunci a sauqaqe

Tsarki | Sallah | Azumi | Zakkah | Hajji



**Dr.Abdullah Bahammam**

tarjama

Muhammad Rabi'u Umar Musa R/lemo

bita

Dr. Muhammad Sani Umar Musa
Shaikh Nura Sani Muhammad

## Sallar Roqon Ruwa

https://www.al-feqh.com/ha



16

# Sallar Roƙon Ruwa

https://www.al-feqh.com/ha


Abubuwan Da Ke cik

- Bayanin Mece ce Sallar Roƙon Ruwa
- Shar'ancin Sallar Roƙon Ruwa
- Lokacin Sallar Roƙon Ruwa
- Wurin Da Ake Yin Sallar Roƙon Ruwa
- Siffar Sallar Roƙon Ruwa
- Wasu Daga Hukunce-Hukuncen Sallar Roƙon Ruwa
- Abin Da Ake So A Yi Yayin Saukar Ruwan Sama


### Sallar Roƙon Ruwa

Ita ce (sallar) neman Allah ya shayar da ruwa bayan fari da ƙarancin ruwan sama

## Dalilim Shar'ancin Sallar Roƙon Ruwa

Sallar roƙon ruwa sunnah ce mai ƙarfi, saboda aikin Annabi (S.A.W) kamar yadda yake a hadisin Abdullahi ɗan Zaid – Allah ya yarda da shi – ya ce, «Manzon Allah (S.A.W) ya fita zuwa wajen sallah, sai ya roƙi (Allah ) shayar da ruwa, ya fuskanci alƙibla, ya juya mayafinsa, ya yi salla raka'a biyu» (Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi).

## Lokacin Sallar Roƙon Ruwa

An shar'anta sallar roƙon ruwa idan ƙasa ta bushe, aka rasa ruwa, ko kuma ruwan ƙoramu da rijiyoyi suka ƙafe da makamancin haka. Ana so ta zama bayan ɓullowar rana da ɗagawarta daidai tsawon mashi. Wannan lokaci galiban ya kasance bayan ɓullowar rana da minti ashirin, kamar lokacin sallar idi.

## Wurin Da Ake Sallar Roƙon Ruwa

A sunna ana yin wannan sallah ne a fili, ba a masallaci ba, saboda haka Manzon Allah (S.A.W) ya aikata, sai dai in da larura.

https://www.al-feqh.com/ha



https://www.al-feqh.com/ha

# Siffar Yadda Ake Yin Sallar Roƙon Ruwa

1. Sallar roƙon ruwa raka'a biyu ce, ba tare da kiran sallah ko iƙama ba, ana bayyana karatu a cikinta

2. Mai sallar zai yi kabbara bakwai bayan kabbarar harama a raka'a ta farko, a raka'a ta biyu zai yi kabbara biyar, banda kabbarar ɗagowa daga sujadda.

3. Mai sallar zai ɗaga hannayensa a kowacce kabbara, sannan ya godewa Allah, ya yabe shi, ya yi salati ga Annabi (S.A.W) a tsakanin waɗannan kabbarori.

4. Bayan gama sallah liman zai yi huɗuba guda ɗaya, zai yawaita istigfari da karatun Alƙur'ani a cikinta, sannan ya yi addu'a da addu'o'in da aka samo daga Annabi (S.A.W) tare da naci da bayyana ƙasƙantar da kai, da nuna buƙata da ƙanƙan ga Allah Maɗaukakin Sarki. Ya ɗaga hannayensa sosai a wajen addu'ar.

5. Liman zai fuskanci alƙibla, ya juya mayafinsa, ya mayar da na ɓangaren dama a hagu, na hagu a dama, ya tsaya ya yi ta addu'a tsakaninsa da Ubangijinsa

## Wasu Daga Hukunce-Hukuncen Sallar Roƙon Ruwa

1. A fara da gabatar da wa'azi da tunatar da mutane kafin a yi ta, a faɗa musu abin da zai tausasa zukatansu, da ambaton tuba daga zunubai, da mayar da kayan zalinci zuwa ga masu su, saboda saɓo sababi ne na hana ruwa, tuba da istigfari kuwa sababi na amsa addu'a da samun alheri da albarka. Hakanan (liman) ya kwaɗaitar da su akan sadaka, saboda sababi ce ta samun rahama.

2. A sanya ranar da za a fita don yin sallar, saboda mutane su shirya.

3. Sunna ne a fita zuwa sallar cikin nutsuwa da tsoron Allah da ƙasƙantar da kai, da bayyana tsananin buƙata ga Allah, saboda haka ba shar'anta yin ado da sanya turare ba saboda ita. Abdullahi ɗan Abbas yana siffata fitar Manzon Allah (S.A.W) zuwa sallar roƙon ruwa ya ce, «Haƙiƙa Manzon Allah(S.A.W) ya fita ba a cikin ado ba, yana mai ƙasƙantar da kai, da komawa ga Allah, har ya zo wurin da ake sallah» (Abu Dawud ne ya rawaito shi).

4. Yawaita neman gafara da addu'a tare da ɗaga hannaye a huɗubar sallar roƙon ruwa.

# Abin Da Ake So Yayin Saukar Ruwa

Ana so a tsaya a cikin ruwa a farkon saukarsa, saboda aikin Annabi (S.A.W) kamar yadda ya zo a hadisin Anas – Allah ya yarda da shi – ya ce, «Ruwan sama ya same mu, muna tare da Manzon Allah (S.A.W). Sai Manzon Allah (S.A.W) ya yaye rigarsa har ruwan saman ya taɓa shi. Sai muka ce, «Ya Manzon Allah (S.A.W) Me yasa ka aikata haka?» Sai ya ce, «Saboda ruwan bai daɗe da rabowa daga Ubangijinsa ba Maɗaukakin Sarki»(Muslim ne ya rawaito shi).



https://www.al-feqh.com/ha

https://www.al-feqh.com/ha



## Ruwa Falala ce Daga Allah Shi Kaɗai

Ya dace ga musulmi ya kudurce cewa ruwa yana sauka ne da falalar Allah da rahamarsa ga bayinsa, ba kamar yadda wasu suke cewa ba «an mana ruwa da tauraro kaza da kaza» wannan shirka ne. Muna neman tsarin Allah Maɗaukakin Sarki.

https://www.al-feqh.com/ha